# Jagora Kan Abun da Mahajjaci Ke Yi Wurin Gudanar da Aikin Hajji da Umra

Daga: Dr. Saleh bin Fawzaan bin Abdullah Al-Fawzaan

بسم الله الرحمن الرحيم

**Gabatarwa**

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin duniyoyi kuma aminci da albarka su tabbata ga Annabi Muhammad, Iyalansa da Sahabbansa.

Cigaba,

Wasu mutanen da ba su taba yin aikin Hajji ko Umrah ba sukan tambaya akai-akai:

"Me za mu yi kuma me za mu ce a lokacin da mu ke gudanar da aikin Hajji da Umrah?"

Don amsa wannan tambayar, na rubuta wannan takaitatta kuma saukakakkiyar huduba saboda mafiyawancin mutane me yiwuwa ba za su iya fahimtar abun da aka rubuta a dunkule ba. Amma duk da haka, zai isa gare su su yi bayanin abun da za su yi a cikin saukakakkiyar hanyar da za a iya fahimta.

Mawallafi

## Ya kai mahajjaci!

Ka jajirce a wurin yin niyya ta gaskiya ga Allah kadai a cikin aikin Hajjinka ko Umrah da dukkan ayukkanka. Kuma ka jajirce a wurin bin Sunnar Annabi (S.A.W), don aikata Hajji, Umrah da duk wasu ayukkan bauta don a karbi dukkan ayukkanka. Ba tare da sharudda biyu ba: niyya ta gaskiya da riko da Sunnah, ba za a karbi ayukka ba. Don haka, ina mai ba ka shawara da ka karanta wadannan bayanan kafin ka fara gudanar da aikin Hajji da Umrah don ka amfana da su.

Ka jajirce don daukar dawainiyar aikin Hajjinka da Umrah ta yin amfani da halattattar dukiya, saboda Hajjin da aka gudanar da haramtattar dukiya ba karbabba ba ce, kamar yadda a ka bayyana a cikin wasu Hadissai.

## Abu na farko: yin Harami

Ka sani, dan'uwana cewa ibada ta farko a wurin aikin Hajji ko Umrah ita ce yin harami. Don haka, ya kamata kasan wuri da lokacin yin harami da kuma abun da ya kamata a yi kafin yin haramin,

ma’anarsa, ayukkan ibadar da ya kamata ka yi a lokacin da ka ke cikin harami. Kari kan hakan kuma, ya kamata ka san abubuwan da ake tunatarwa a yi a lokacin harami da kuma bayansa, da kuma abubuwan da aka haramta a yi a lokacin da a ke cikin harami. Don haka sai ka kula da abubuwan da ke tafe:

1- **Wurin yin harami:**

Annabi (S.A.W), ya bayyana wuraren da mahajjaci zai yin harami, shi ne a duk lokacin da ya ke wucewa a daya daga cikin wadannan wurare:

1) Dhul-Hulaifah wanda ake kira da suna Abyaar Ali (watau rijiyoyin Ali) a halin yanzu. Shi ne Miqat (watau wurin da aka bayyana) na mutanen garin Madina da duk wanda zai wuce ta wurin ko dai ta kasa ko a kan jirgin sama.
2) Al-Juhfah wuri ne da ke kusa ga Rabegh a hanyar teku. A halin yanzu, mutane na yin harami daga Rabegh wanda bai kai wannan Miqat ba da ‘yar tazara kadan. Wannan shi ne Miqat na mutanen da ke fitowa daga

yawancin kasashen da ke Maghreb watau kasashen Sham, Labanon da Isra'ila da kuma Misirah da kuma duk wanda zai wuce su ta kasa ko kan jirgin sama.

3) Yalamlam (wanda ake kira da suna As-Sa'deyya a halin yanzu). Nan ne Miqat na mutanen Yamen da duk wanda zai biyo ta wannan hanyar.
4) Qarn Al-Manazil (wanda ake kira As-Sayl a halin yanzu). Shi ne Miqat na mutanen Najd da duk wanda zai biyo ta wannan hanyar a kasa ko kan jirgin sama.
5) Zat 'Irq nan ne Miqat na mutanen kasar Iraki da duk wanda zai biyo ta hanyar a kasa ko kan saman jirgi.
6) Mutanen da ke zaune a wasu wurare amma kuma gidajensu na kusa ga garin Makka, za su yi harami ne daga gidajensu. Su kuma mazauna garin Makka, su yi haraminsu daga Makka idan aikin Hajji ne za su yi. Amma za su tafi wuri na farkoda ke bayan unguwa maitsarki ta garin Makka, don yin haramin Umrah. Haka kuma, duk wanda ke biyo wa

ta wadannan Miqatan ba tare da yin haramin aikin Hajji ko Umrah ba, kuma yayi niyyar yin aikin na Hajji ko Umrah, amma kuma ya yi harami daga wurin da ya ga dama. Ba a yarda ba ya wuce wannan wurin ba tare da ya dauki harami ba. [1]

## 2- Lokacin yin Harami :

Ana iya yin harami a cikin watannin da Allah Ya ambata kamar haka: ﴿الْحَجُّ أَشْهُرٌ مَّعْلُومَاتٌ﴾ [2: 197] . Su ne watannin Shawwal, Dhul-Qi'dah da kuma kwanaki goma na Dhul-Hijjah. Duk wanda ya dauki harami kafin wadannan watannin, to haraminsa ba karbabbe ba ne kamar yadda mafiyancin malamai ma su bayar da fatawa suka bayyana.

Wanda duk ya yi harami kuma ya yi tsayuwar Arafah kafin wayewar garin goma ga watan Dhul-Hijjah, to Hajjinsa karbabba ce. Amma an yarda a dauki harami don yin aikin Umrah a kowane lokaci.

---

[1]Wanda duk bai wuce ta wannan Miqat ba, sai ya yi Harami a lokacin da ya ke hannun riga da ita Miqat din.

**3- Abubuwan da ya kamata a yi kafin yin Harami:**

In ka yi niyyar yin harami, an so ka yi wadannan abubuwan da ke biye don shirin yin Haramin:

A. Datse gashin baki, yankan farce (kumba), tsunkar gashin hamutta da kuma aske gashin mara. Amma idan wani daga cikin wadannan wuraren ba ya bukatar askewa, to sai ka bar sa yadda ya ke. Idan kuma ka yi aski ba da dadewa ba, to wannan ma ya wadatar.

B. jiki baki daya don kawar da duk wani datti, amma ka tabbata kana wankan ba a idon mutane ba. Kuma idan ba ka halin yin wankan, sai ka bari don ba dole ba ne.

C. Dole ne mahajjaci namiji ya cire duk wata suturar da ke manne a jikinsa kamar irin su mayafi, riga da safa. A maimakon hakan, sai ya sa Izar (suturar da ake sawa a kasan kugu)

da kuma Rida (zanen da ke rufe saman jiki), kuma an so dukkan wadannan suturun su kasance farare kuma masu tsafta, ko dai sabbi ko kuma tsoffi. Kuma an yarda ya sa kowane irin nau'in takalmin da ba ya mannewa a kafa, an kuma yarda ya sa silifa wadanda ba za su wuce duddugensa ba, ba tare da ya sa safa ba.

Ita kuma mahajjaciya, an so ta cire Burqu ko Niqab (Marufin fuska) ta kuma rufe fuska a maimakon hakan da wani bangaren Khimaar dinta (hijabin da ya rufe fuskarta) don boye fuskarta daga ganin duk wanda ba Maharaminta ba (watau duk wani namijin da aure bai haramta ba a tsakanita da shi). Ba ta da laifi idan abun da ta rufe fuskarta ya tabi fuskarta din. Da ya ke babu bukatar sa rawani ko wani abu mai kama da shi don hana abun rufe fuskar ya taba fuskarta kamar yadda wasu mata su ke yi; al'amarin da ya saba ma aikin Sunnah**.**

Mace za ta cire safar hannunta. An yarda ta sa komi in ban da abun da zai rufe fuskarta ko safar hannu ba, muddin dai abun za ta sa ba wani kayan yin ado bane. Babu wata kalar haramin da aka tilasta

ma mace sawa, kamar yadda wasu su ke kuskuren cewa dole ne mace ta daura koren harami, wanda wannan zancen ba ya da hurumi a tsarin Shari'ah. Haka kuma, wasu suna kuskuren imanin cewa dole ne mata su sa fararen kaya. Shi ma ba a yarda da haka ba, don yin hakan wani bangare ne na kwaikwayen maza.[1]

D. Bayan yin wanka, mahajjaci namiji zai shafa turare a jikinsa kawai, amma kar ya shafa ma suturar haraminsa. Sannan ya yi Harami. An yarda mata su yi amfani da turaren da kamshinsa ba ya da karfi [wanda maza ba za su ji kamshinsa ba].

**4- Ma'anar Harami:**

Bayan kammala dukkan shirye-shiryen da aka ambata a bayanin da ya gabata, to ka yi Harami ke nan. Harami na nufin yin niyyar fara ibadar da mutum ke da kudurin gudanarwa. Da zarar kana da wannan niyya, ka yi Harami ke nan ko da kuwa ba

[1] Sai ta yi Harami da kayanta na al'ada, amma ban da na yin ado.

ka furta niyyar ba da fatar baki. Ya fi kyau mutum ya yi Harami bayan ya gabatar da daya daga cikin sallolin farilla. In ba lokacin sallar farilla ba ne, to sai mutum ya yi sallah raka'ah biyu kafin yin Haramin, yin hakan na da kyau, sai dai in har lokacin yana daya daga cikin lokuttan da aka haramta yin sallah, misali; bayan wayewar safiya da kuma bayan sallolin tsakiyar rana. A duk wadannan lokuttan za ka yi Harami ne ba tare da yin sallah ba. Idan wani ne ya umurce ka da ka aiwatar masa da aikin Hajji ko Umrah, to babu laifi a kanka don ka ce, "Labayka Allahoma 'an folan (Ya Allah! Ga ni gare ka [ina bautarka] a madadin wane)".

## 5- <u>**Nau'o'in ayukkan Hajji da mahajjaci zai iya zaba daga cikinsu**</u>:

<u>Aikin Hajji na da nau'ukka ukku</u>:

(watau Tamattu', Qiran da Ifrad); amma wanda ya fi daga cikinsu shi ne Tamattu sannan Qiran na bi ma sa, sai kuma na karshensu Ifrad.

Hajjin Tamattu: shi ne wanda mahajjaci zai yi niyyar yin aikin Umra kawai a cikin watannin

gudanar da aikin Hajji (watau Shawwal, Dhul-Qidah da kuma kwanakin goma na farko na watan Dhul-Hijjah) a Miqat. Bayan ya gudanar da aikin Umrah, sai ya ajiye Harami. Bayan nan, sai mahajjaci ya bayyana niyya a cikin garin Makka ta yin ibadodin aikin Hajji, ya kuma yanka dabba (sadaukar da dabba) don Tamattu' idan dai har ba ya daga cikin mutanen da ke zaune a yankin Masallaci Maitsarki.

Hajin Qiran: shi ne wanda mahajjaci ke ayyana niyyar yin aikin Hajji tare da Umrah a lokaci daya da yin Harami daya a Miqat, ko mahajjaci zai yi Haramin Umrah ne da farko, sannan ya dora niyyar yin aikin Hajji a kan niyyar kafin yin Dawafi. Za ka ci gaba da zama cikin Haraminka har lokacin yin jifar shedan ranar Idi, ka yi aski kuma ka yanka dabba a matsayin sadaukarwa kamar dai yadda mahajjacin Tamattu' zai yi.

Ifrad: shi ne yin Haramin aikin Hajji kawai a Miqat, da kasancewa a cikin Haramin har zuwa lokacin yin jifar shedan a ranar Idi, sannan ka yi aski. Duk da haka, a wannan nau'in na Hajji, babu dole gare ka na

yanka dabba. Za a yi cikakken bayani kan haka a nan gaba.

6. **Abubuwan da a ke son a fadi a lokacin Harami da kuma bayan Harami:**

A. Game da Tamattu', an so a ce “Ya Allah! Na yi niyyar Harami don yin aikin Umrah sannan kuma in yi aikin Hajji (a matsayin Tamattu’). Ka saukaka man shi, kuma Ka karba man” ko kuma ka ce “Labayka Allahumma Umrah Mutamatti’an biha ilal-Hajj” wanda ya ke nufin cewa “Ya Allah! Ga ni zan gudanar da aikin Umrah sannan in yi Hajji [a Tumattu’]”.

B. Game da Qiran, an so a ce: “Ya Allah! Na yi niyyar yin Harami don gudanar da ayukkan Umrah da Hajji” ko “Labayka Lahoma Umrah wa Hajji” wanda ke nufin “Ya Allah! Ga ni zan gudanar da ayukkan Umrah da Hajji a tare gaba daya”

C. Game da Ifrad, an so a ce: “Ya Allah! Na yi niyyar yin Harami don gudanar da aikin

Hajji” ko “Labayka Allahoma Hajji” wanda ya ke nufin “Ya Allah! Ga ni zan gudanar da aikin Hajji.”

Idan ba ka da lafiya kuma kana tsoron cewa me yiwuwa ba za ka iya gudanar da aikin Hajji ko Umrah ba, an yarda ka ce a lokacin da ka ke yin Harami: “In har wata matsala ta sa na kasa kammala aikin Hajjina ko Umrahta, matsayin ibada ta ya kasance a dai-dai wurin da matsalar ta same ni.” Kan wannan sharadin, in har ka kasa kammala aikin Hajjinka, za a dauke ma Haraminka, kuma ba za ka yanka dabba ba saboda kariyar ayyana wannan addu’ar tun daga farko.

Bayan yin harami, sai ka karanta Talbiyyah kamar haka: “Labayka Allahoma Labayk, Labayka la Shareeka Laka Labayk Ina Alhamda Wani’mata Laka wal Mulk La shareeka Lak” (Ya Allah, ga ni a nan. Gani a nan. Hakika Alheri da Mulki duka naKa ne, kuma ba ka da wani abokin tarayya)." Namiji zai fadi haka da karfi, amma kuma mace za ta fadi a cikin murya marar karfi.

**<u>Muhimmin Bayani</u>**:

**<u>Na farako</u>**: idan mace na cikin jinin haila ko jinin biki kafin yin Harami, to sai ta yi wanka ta kuma tsaftace jikinta sannan ta yi niyyar yin Harami, za ta kasance a cikin Haraminta kuma ta gudanar da dukkan ibadodin aikin Hajji kamar kowa, amma ban da Dawafi, wanda za ta jinkirta shi har sai ta yi tsarki. In ta yi niyyar yin Tamattu' ne, kuma ranar Arafah ne amma ba ta yi tsarki ba, to sai ta yi niyyar aikin Hajji kuma ta gudanar da shi tare da Umrah, kamar yadda ya ke a aikin Hajjin Qiran. Sannan ta tafi Arafah ta yi dukkan ibadodin aikin Hajji, amma ban da Dawafi da Sa'yi (tafiya a tsakanin Safa da Marwah) wanda za ta jinkirta har sai ta yi tsarki. [1]

**<u>Abu na biyu</u>**: mahajjacin da ke kan jirgin sama zai yi Haraminsa ne a cikin jirgi, a lokacin da jirginsa yake wuce wa daya daga cikin Miqat. Ba a yarda ya jinkirta yin Haraminsa ba har sai ya isa filin

[1] Haramin yaro (da bai balaga ba) ingantacce ne, ko na Hajii ne ko Umrah. Idan dan karamin yaro ne da ke gabanin balaga, sai yay i wa kansa niyya, amma in karami ne sosai, sai mai kula da shi yayi masa niyyar. Kuma ya hana shin duk wani abun da Harami ya haramta.

jirgin saman Jeddah, sai dai mutanen garin na Jeddah ko kuma wanda ke da niyyar yin aikin Hajji a lokacin da yake cikin garin na Jeddah.

In ya yi wanka, ya tsaftace jikinsa ya sa Izar a karkashin kayan da yake saye da su na al'ada kafin ya shiga jirgi, a nan, zai fi kyau ya tube kayan nasa da ke jikinsa, ya sa Rida' ya kuma yi Haraminsa a lokacin da ya ke wuce Miqat, ko ya ke kusa da Miqat.

Idan ba ya da kayan shiga Harami, an yarda ya bar wandon da ke jikinsa, to amma ya dauki mayafinsa ya yafa a bayansa da kuma gabansa don yin Harami. Amma da zarar ya isa filin jirgi sai ya hanzarta sa kayan Haraminsa, ya kuma cire wandon da ke saye a jikinsa.

Amma ita mace ba dole ba ne ta sa wasu kayyadaddin kayan Harami. Sai dai ita ma za ta yi Haraminta a lokacin da ta ke cikin jirgi. Amma za ta cire marufin fuskarta, sannan ta rufe fuskarta da wani sashen hijabin da ke kanta, kamar dai yadda

anka ambata a bayanin da ya gabata. Kuma kari kan hakan shi ne mace za ta cire safar dake hannunta. [1]

**Abu na ukku**: wasu mahajjata na da al'adar daukar hoto don tarihi. An haramta yin wannan al'adar saboda dalilai biyu: [2]

Na farko: daukar hoto aikin rashin da'a ne kuma aikata babban zunubi.

Abu na biyu: Wannan aikin yana daga cikin ayukkan Riya (kankanba) saboda ta hakan, mahajjaci na son jama'a su ga hotonsa a lokacin da yake cikin Harami. Aikin Riya na wargaje ayukkan alheri. Don haka dan'uwa Musulmi sai a kiyaye.

**Abu na hudu**: Ba wanda anka ba izinin yi ma wani aikin Hajji ko Umrah, ba tare da ya yi nasa aikin Hajjin ko Umrah ba.

**Abu na biyar**: wasu mahajjata maza na da al'adar bude kafadunsu na dama a lokacin da suke

---

[1] Kuma ta rufe fuskarta [daga ganin mazan] da wani sashen suturarta ko mayafinta.

[2] Don haka, ba dai-dai ba ne a fara aikin Hajji da yin zunubi.

cikin Harami. To wannan kuskure ne, an yarda ayi hakan ne kawai a lokacin yin.[1]

**7.** Al'amurran da aka hana bayan an yi Harami:

A. Bayan an yi Harami, an hana ma mahajjata maza da mata shafa turare a jikinsu ko suturarsu. Kari kan hakan kuma, an haramta masu ko da niyyar sunsuna turare ne, ko kuma amfani da duk wani nau'in abu mai kamshi, abinci ne, abinsha ne, man shafawa ne ko kuma sabulu ne, duk dai an hana amfani da irin wadannan abubuwan da ke da kamshi.

B. An haramta ma mahajjata maza da mata aske ko datse gashin kai ko na jiki. Haka kuma an haramta ma su yankan farce (kumba)

C. An haramta ma mahajjata maza da mata yin farautar dabbar da ke rayuwa a kasa ko su

[1] Abun da a ke nufi a nan shi ne Dawafin da a ke yi daga sauka, ko dai Dawafin Qodum ko na Umrah.

taimaka ma wani ta kowace hanya don ya yi farautarsu, ta hanyar yi ma sa jagora ko kuma nuna ma sa dabbobin da zai farauta da sauransu.

D. An haramta ma mahajjata maza da mata yin jima'i, (tsakanin ma'aura) ko kuma neman aure ko yin baiko ko yin duk wata magana game da daya daga cikin wadannan al'amurran da aka bayyana.

E. An haramta ma mahajjata maza rufe kansu da wani abun da zai taba kan, kamar su rawani, hula da ire-irensu. Babu laifi a gare su don sun yi amfani da lema ko wani abu mai kama da ita don samar da inuwa.

F. An haramta ma mahajjata maza sa suturar da ke mannewa a jiki kamar irinsu riga, safa da sauransu. Duk da haka, babu laifi a kansu idan sun daura kwagirin sa kudi a kugunsu don amfani da su wurin biyan bukatu. Kuma an yarda mahajjata maza su sa madubin ido

ko agogo [1] da takalmi sandal da gajerun takalmin da ba za su wuce dudduge ba. Amma takalmi sandal sun fi rufaffin takalmi.

G. An haramta ma mahajjata mata su sa Burqu' ko Niqab da kuma kowane irin abun da aka dinka don rufe fuska. Kari kan hakan kuma, an haramta ma su sa safar hannu wadda ta ke anyi ta ne da zaren ulu, auduga ko wani abu maikama da su don sawa a hannu.

.**<u>Kura-kuran da ake aikatawa a cikin Masallatan At-Tan'eem Al-Je'raahah:</u>**

1- Masallacin At Tan'eem:

Ba da dadewa ba, mahajjata da dama sukan tafi Masallacin Tan'eem da imanin cewa umurnin Shari'ah ne yin sallah a wurin kafin zuwa Masallaci Mai tsarki. Wasu mahajjatan ma sukan rasa yin Harami daga Miqat da aka ambata wanda suka wuce don kawai su yi Haramin a Masallacin na Tan'eem. Sauran mahajjatan da ke zaune a garin Makka sukan

[1] Da zobe

tafi Masallacin na Tan'eem akai-akai don yin niyyar Haramin Umrah. Dalilin yin wadannan ayukka shi ne imanin da wasu mahajjata suka yi na cewa Masallacin na Tan'eem yana da wata daraja ta musamman wadda ta sa ake ziyarar sa. Wannan shi ne dalilin da ya sa tunatar da Musulmi ya wajaba kan cewa wannan Masallacin baya da wani muhimmancin da yafi na sauran Masallatai. Don haka, yin tsinke zuwa wannan Masallaci da wannan imanin a zuciya bidi'a ne, kamar yadda Annabi (S.A.W) yace: "Duk wanda ya yi wani aiki da ba mu umurce sa da yi ba, to ba za a karbi aikin nasa ba."

Zarcewa zuwa wannan Masallacin da ziyartar sa akai-akai ba aiki ne na sunnar Annabi Muhammad (S.A.W) ba, ko Sahabbansa. A gaskiya ma, ba a lokacin rayuwar Annabi (S.A.W) ba ne aka assasa wannan Masallacin, amma an gina shi ne a bayan rayuwarsa aka kuma sa ma sa suna Masallacin Aisha. Dalilin sa ma shi sunan Aisha shi ne saboda daga nan ne ta yi Haraminta.

Wannan tsohon tarihi ne. a lokacin rayuwar Annabi (S.A.W), Aisha ta roke shi ya ba ta izni ta yi aikin Umrah bayan Hajji saboda ba ta yi aikin

Umrah ba kafin Hajji, don a lokacin tana cikin al’ada. Bayan ta roke Annabi (S.A.W) iznin yin Umrah sai ya umurce ta da ta tafi Tan’eem ta yi niyyar yin Haramin Umrah saboda a nan ne wuri mafi kusa da ke wajen unguwa maitsarki na birnin. Duk da yake niyyar yin Harami a wurin yafi sauki a gare ta, wannan ba ya na nufin Masallacin na da wani muhimmanci na musamman ba da yafi sauran wuraren da ke wajen unguwa maitsarki. Tunanin da wasu ‘yan tsirarun mutane ke yi na cewa wannan wurin yafi ko’ina muhimmanci babu shakka wannan kuskure ne.

Zuwa wannan masallaci da wannan imani a zuciya Bidi’ah ne, kuma in wani ya ki yin Harami a Miqat don kawai ya yi shi a Tan’eem, zai aikata abun da aka hana kuma ya bar daya daga cikin wajibban Hajji ko Umrah. Akan haka, zai yanka dabba (watau tunkiya) a Makka a matsayin sadaukarwa, kuma ya raba namanta ga mabukatan da ke wurin. Ta hanyar barin niyyar yin Harami a Miqat din da aka bayyana, mahajjaci ya aikata zunubi wanda ke bukatar yin tuba tare da yanka dabbar da aka ambata a bayanin da ya gabata.

Wanda duk ya bar ziyarar Masallaci Mai tsarki bayan ya isa Makka, kuma ya tafi Masallacin Tan'eem don yin sallah a can, ya aikata bidi'ah wadda take da mummunan zunubi. Dalilin haka kuwa shi ne, abun da anka umurci kowane mahajjacin da ke cikin Harami wanda ya isa Makka shi ne ya ziyarci Masallaci Mai tsarki, ya yi Dawafi sannan ya yi Sa'y a tsakanin Safa da Marwah in aikin Umrah ne ya ke yi, ko ya yi Dawafin Qudom (daga isa) in niyyar Hajjin Qiran ko Ifrad ce ya dauka. Bai kamata mahajjaci ya tafi Tan'eem ko wasu masallatai ba. Barin garin Makka zuwa Tan'eem don yin Haramin Umrah kafin ko bayan aikin Hajji, kai koma a wane irin lokaci ne ba wai Hajji kadai ba, abu ne da ya saba ma abun da a ke so. Saboda tsayawa a Masallaci Mai tsarki, yin sallah da yin Dawafi a wurin ya fi barin garin Makka don yin Haramin Umrah a Tan'eem ko wani wurin na daban, kuma Allah ne Yafi kowa sanin abun da yafi dacewa.

**2-** Masallacin Je'raanah:

Je'raanah (wanda ake kira Je'erraanah) wuri ne da ke tsakanin Makka da Ta'if, amma yana kusa ga

Makka. Wannan wurin da masallacin da ke wurin ba wasu wurare ne na musamman ba ko masu wata darajar da tafi ta sauran wuraren da ke wajen unguwa maitsarki kamar yadda wasu mutane suka yi imani. Annabi (S.A.W) ya yi Harami a wannan wurin a kan hanyarsa ta dawowa daga Hunain. Annabi (S.A.W) ya yi Harami daga Je'raanah saboda ya na da niyyar yin Umrah a wannan wuri a kan hanyarsa ta dawowa garin Makka.

A zahiri dai Annabi (S.A.W) da Sahabbansa ba su yi niyyar Harami a Je'raanah ba ko sallah a wurin. Abun da wasu mutane ke yi na barin Makka su tafi Je'raanah su yi Harami ko sallah a wurin ba Sunnar Annabi (S.A.W) ba ce, kuma ba ta Sahabbansa ba ce. Bugu da kari ma, ba wani daga cikin malaman da ake girmamawa da ya yarda ko ya amince da yin hakan; hasalima wasu 'yan tsirarun mutane ne su ke aikata hakan, su a ganinsu Sunnah ce, wanda kuma ba haka ba ne. Saboda Annabi (S.A.W) ya yi Harami ne a wurin a lokacin da yake kan hanyarsa ta zuwa Makka. Koyarwar Sunnah ga duk wanda ke shiga Makka ta hanyar Ta'if da makwabtanta shi ne su yi

Harami daga Je’raanah ko duk wani wurin da suke wucewa dake bayan unguwa mai tsarki.

**Abu na biyu: Me ya kamata mahajjaci ya yi daga saukarsa Makka?**

1- Mahajjacin Tamattu':

Daga sauka Makka, mahajjacin da ya yi niyyar yin Hajjin Tamattu’ zai gabatar da duk ibadodin Umrah, ya fara da yin Dawafin (zagayen) dakin Ka’abah sau bakwai; kowane zagaye zai fara ne daga Bakin Dutse kuma ya kare a wurin. Bayan kammala zagayen sau bakwai, sai ya yi sallah raka’a biyu, an so ya yi ta a Maqam Ibrahim (wurin da Annabi Ibrahim ya tsaya a lokacin da yake gina dakin Ka’abah). In hakan bai samu ba, mahajjaci na iya yin sallar a kowane wuri cikin Masallacin. An so a sha ruwan Zamzam sannan a wuce zuwa wurin yin tafiyar Safa a tsakanin Safa da Marwah maya bakwai, kowace maya za a fara ta ne daga Marwah a kare da Safa, kuma za a ci gaba ne ba tsayawa har sai an kammala maya ta bakwai.

Bayan wannan, sai mahajjaci namiji ya yi saisayen gashinsa ita kuma mace za ta datse nata gashin dai-dai tsawon kan yatsa (farce). Bayan gama wadannan ayukkan, shi ke nan mahajjaci ya kammala aikin Umarah, kuma ya sauke Haraminsa, daga nan yana iya aikata abubuwan da Harami ya haramta ma sa yi.

A nan sai a kula cewa ginshikan Umrah su ne; Dawafi da Sa'y kuma wajibanta su ne yin Harami daga Miqat da aka bayyana tun da farko da kuma yin aski ko datse gashi.

## 2- **Abun da Mahajjacin Qiran ko Ifrad ya kamata ya yi daga saukarsa Makka:**

Daga sauka Makka, an so mahajjacin da ya yi niyyar yin Hajjin Qiran ko Ifrad ya yi Dawafin Qudom sau bakwai sannan ya yi sallah Raka'a biyu. Bayan ya kare, an ba shi izinin ya hanzarta yin Sa'y na Qiran in Hajjin Qiran ne ya ke yi, ko kuma Sa'y na Hajji in Ifrad ne ya ke yi. Kuma an yarda ya jinkirta shi bayan yin Dawafin Ifaadhah. Bayan wannan,

mahajjaci zai kasance cikin Harami har zuwa ranar Idi.

**Muhimman abubuwan kula:**

Da farko: sharuddan dake inganta Dawafi su ne niyya, tsarki da kuma rufe al'aura (watau tsiraici, sashen jikin da ya kamata a rufe a lokacin da a ke yin sallah). Ana ayyana yin niyya ne a cikin zuciya, kuma ba a furta wa da baki. Sharuddan inganci su ne kammala zagaye bakwai (Dawafi) wanda kowane zagaye zai fara ne daga Bakin Dutse ya kuma kare a wurin da kuma zagayen Hijr Isma'eel. Idan mahajjaci ya shiga ciki ba zagaye ba, to Dawafinsa bai inganta ba, saboda mafiyawancin sashen Hijr mallakar dakin Ka'abah ne.

Abu na biyu: an so mahajjata maza su bude kafadarsu ta dama a lokacin yin Dawafin Umrah da Dawafin Qudom, kuma su yi sassarfa a zagaye ukku na farko, in har yana iya dai-daita sawunsa, ana kiran yin hakan Ramal.

Abu na ukku: Dawafi da Sa'y ba su da wata addu'a ta musamman da a ke karantawa a lokacin da

a ke yin su, amma mahajjaci zai iya rokon duk wani abun da yake nema ga Allah. An yarda ya yabi Allah, ya karanta Takbeer "Allahu Akbar (Allah Mai Girma), da kuma yin Tahleel "La Ilaha Ila Allah (babu abun bauta ma sai Allah)" . Haka kuma, ya na iya karanta wasu ayoyin Al'qurani Maitsarki. Ba a yarda ya rika kutsawa da karfi ba yana turin mutane don ya kai ga Dutse. Duk da haka, idan zai iya kaiwa gare shi, sai ya taba kuma ya sumbace shi. Amma idan ba zai iya ba, ya isa idan ya nuna Dutsen da hannunsa a lokacin da yake hannun riga da shi. Daga nan sai ya taba Kusurwar Ka'abah ta Yamaani ba tare da sumbatar ta ba. Amma idan ba zai iya kaiwa gare ta ba, sai ya tafiyarsa ba tare da ya nune ta ba.

Abu na hudu: daga cikin ingancin Sa'y akwai yin niyya, yin Sa'y bayan an yi Dawafi da kuma kammala yin tafiya bakwai wadanda kowannen su za a yi shi ne a tsakanin Safa da Marwah.

Abu na biyar: in lokacin sallolin jam'i na farilla ne kuma mahajjaci na cikin yin Dawafi ko Sa'y, to sai ya dakata don kar ya rasa sallar jam'in.

Bayan kammala sallar sai ya ci gaba daga kewayen. [1] da ya tsaya

## 3- Abun da ake yi a ranar Tarwiyyah:

Ranar Tarwiyyah ita ce ranar takwas ga watan Dhul-Hijjah. A wannan ranar a ke so Mutamatte' wanda ya ajiye Haraminsa bayan gudanar da aikin Umrah ya sake komawa cikin Haramin nasa don yin Hajji da rana. Zai yi hakan ne kamar yadda ya yi a lokacin da yake yin Harami a Miqat, watau yin wanka, tsarkake jiki da kuma shafa turare. Sannan ya yi Harami daga wurin da yake da zama. Ga mahajjattan da ke gudanar da aikin Hajjin Ifrad da Qiran, su dama ko can suna tare da Haraminsu da suka yi tun a Miqat. Dukkan mahajjata za su tafi Mina kafin tsakiyar rana. Ba za su tafi Masallaci Maitsarki ba don yin Dawafin dakin Ka'abah. A maimakon hakan, za su fito daga gidajensu don zuwa Mina. Su yi sallar rana, sallar maraice da kuma sallar huturu da kuma sallar dare a wurin cikin lokuttan yin su, kuma su gajarce sallolin da ke da raka'ah hudu zuwa raka'ah biyu. Za su

[1] Watau daga farkon wannan zagayen.

kashe daren tara ga wata a Mina, kuma su yi sallar subahin a wurin. Kashe dare a Mina Sunnah ce; amma kuma babu laifi ga wanda bai yi hakan ba. Wanda duk ke zaune a Mina kafin ranar Tarmiyya zai yi Haraminsa ne a Mina da rana kamar yadda sauran mahajjata suke yi, kuma ya tsaya a nan wurin da yake da zama.

## 4- Tsayuwar 'Arafah da kuma abun da ake yi a wannan ranar:

A lokacin da rana ta fito, ranar tara ga wata, dukkan mahajjata za su tafi Arafah cikin natsuwa suna yin Talbiyyah. Bayan sun isa Arafah, za su tsaya ne a duk wurin da suka samu damar tsayawa a cikin harabar wurin. Ba dole ba ne sai an tafi kusa ga dutsen, a gane sa ko a hau kansa. A lokacin da rana ta yi Zawaali (ta gota bayan sa'o'in rana), sai su yi sallar rana da kuma maraice tare, su gajarta kowace sallar daga raka'a hudu zuwa biyu. Za a yi kiran sallah daya ne ga dukkan sallolin biyu, kuma kowace sallah za a yi mata ikamar ta. Bayan haka, za su kashe lokacinsu suna yin tasbihi da addu'o'i zuwa ga Allah har sai rana ta fadi. Da rana ta fadi sai

su bar Arafah zuwa Muzdalifah. Wanda duk ya bar Arafah kafin faduwar rana zai sake komawa wurin ya tsaya har sai rana ta fadi, kuma in har bai yi hakan ba, to zai yanka dabba a matsyin fansar kai. Idan mahajjata suka bar Arafah bayan faduwar rana, za su kasance a cikin halin natsuwa da muhimmantawa. Kari kan hakan kuma, za su karasa lokacinsu ne suna yin Talbiyya da Istighfar (rokon gafara ga Allah).

**Muhimmin abun kula:**

Ya isa ga duk wanda ya kai Arafah bayan faduwar rana ya tsaya a wurin na wani lokaci. Tsayuwar Arafah na karewa ne bayan ketowar alfijir na safiyar Idi.

**5- Kashe dare a Muzdalifah:**

A lokacin da mahajjata suka isa a Muzdalifah, za su yi sallar huturu da ta dare a tare, za a yi masu kiran sallah daya ne da kuma Iqaamah biyu. Za su gajarta sallar dare daga raka'ah hudu zuwa biyu. Sannan su kashe dare a wurin. Bayan dare ya raba, mahajjata masu rauni kamar mata da

kananan yara da tsofaffi da masu kula da su an yarda da su bar wurin zuwa Mina. Amma mahajjata masu jini a jiki, wadanda babu wanda suke kula da shi, ya na da kyau su tsaya a Muzdalifah har ketowar alfijir. Su yi sallar asubahin a lokacin yin ta, sannan su ci gaba da yin addu'o'i ga Allah har rana ta keto. Bayan fitowar rana, sai mahajjata su wuce zuwa Mina. An haramta ma kowane mahajjaci barin Muzdalifah kafin rabawar dare, kuma duk wanda ya yi hakan, to ya aikata zunubi kuma sai ya yanka dabba a matsayin fansar kai. Saboda kashe dare a Muzdalifah daya ne daga cikin wajibban aikin Hajji, kuma karancinsa shi ne tsayawa a wurin har dare ya raba. Ya isa idan mahajjaci ya sauka a Muzdalifah bayan dare ya raba koma in ya samu ya kashe dare a wurin.

## 6- <u>Ibadodin aikin Hajji a ranar Idi</u>:

Alokacin da mahajjata suka bar Muzdalifah zuwa Mina, za su tsinci kankaru guda bakwai a Muzdalifah ko kuma a kan hanyarsu ta zuwa Mina. Girman kowace kankara ya kasance kamar kwayar gida. Da sun isa Mina an so su fara jifar shedan

(babban ginshiki). Mahajjaci zai jefa kankaru bakwai, daya bayan daya, yana mai daga hannunsa yana cewa "Allahu Akbar (Allah Mai Girma)". Kamata ya yi kowace kankara fada a cikin wurin da aka shata. Lokacin jifar shedan na farawa ne tun daga rabawar dare har zuwa faduwar ranar goma ga wata. An so mahajjatan da ke da jini a jiki su yi ta su jifar bayan wayewar garin goma ga wata. Bayan jifar shedan, sai mahajjatan da ke yin Hajjin Tamattu' da Qiran su yanka dabba (hadaya).[1] Lokacin yanka zai fara ne daga wayewar garin ran. ar Idi ya kuma kare da faduwar ranar sha ukku ga wata, watau ranar Idi da kuma kwanakki ukku bayanta. An so mahajjaci ya ci wani abu daga abun da ya yanka, kuma ya yi sadaka da wani.

Bayan yanka dabba, sai mahajjaci namiji ya aske gashin kansa ko ya datse gashin, ita kuma mahajjaciya mace za ta datse kwatankwacin kan yatsa ne kawai na gashinta. Da jifar shedan da kuma aske gashi a wannan ranar, shi ke nan mahajjaci ya sauke Haraminsa, kuma yana da damar aikata duk

[1]Watau daga farkon wannan zagayen.

wani abun da Harami ya haramta masa, kamar sa suturar da ke mannewa a jiki, shafa turare da duk sauran al'amurra in ban da jima'i a tsakanin ma'aurata, wanda aka halatta yi kawai bayan an kammala Dawafin Ifaadhah. Bayan jifar shedan, yankan dabba da datse gashi, mahajjaci na iya komawa Makka a ranar Idi don yin Dawafin Ifaadhah da Sa'y ga masu Hajjin Tamattu' ko Qiran ko Ifrad in mahajjaci bai yi Dawafin Qudum ba. Yin Dawafi a wannan ranar yafi, saboda an yarda mahajjaci ya jinkirta shi. Lokacin yin wannan Dawafin na farawa ne tun daga rabawar daren ranar kuma lokacin ba ya da iyaka. Duk da haka, zai fi kyau idan ba a jinkirta shi ba bayan kwanaki ukku na Tashrreq (watau ranakun 11, 12 da 13 na Dhul-Hijjah)

**Muhimman abubuwan kula**:

1) Kamata ya yi ibadodin hudu a gudanar da su jere da jere kamar haka: jifar shedan sai yankan dabba, sannan yin aski ko datse gashi, sai kuma Dawafin IFaadhah. Yin Sa'y bayan an yi Dawafin Ifaadhah ya fi, amma

babu laifi ga mahajjaci idan ya gabatar da daya daga cikin wa'yannan ibadodi kafin yin dayan. [1]

2) Kammala ibadodi ukku na jifar shedan, aske gashi da Dawafin Ifaadhah da Sa'y [idan har ba a yi ba] ya ba mahajjaci iznin aikata duk abun da Harami ya haramta yi ciki har da yin jima'i a tsakanin m'aurata.

3) Hadaya (yankan dabba) yana da sharudda iri daya da Udhhiya (sadaukarwar layyar Idi). Dole ne ya kasance dabba ta isa; matashiyar tunkiyar da ta cika watanni shidda, tsohuwar tunkiyar da ta cika shekara daya, shanuwar da ta yi shekaru biyu ko kuma rakumin da ya yi shekaru biyar. Za a yi layyar tunkiya don sadaukarwa ga mutum daya ne kawai, yayin da mutane bakwai za su iya tarayyar sadaukarwa ga yankan shanuwa ko rakumi. Dabbar da za a yanka ta kasance ba ta da wani lahani kamar rashin lafiya, matukar tsufa, makanta, gurgunta ko rasa daya daga

[1]Wataua yi dawafi kafin jifr shedan ko yin aski kafin Dawafi.

cikin kafafunta hudu. Ba a yarda mahajjaci ya yanka dabbar hadayarsa sannan ya sa rashin kula ba; a'a zai ci wani sashe daga naman dabbar ne kuma ya raba wani naman ga mabukata, ko kuma ya yanka dabbar ya ba su naman gaba daya. An yarda mahajjaci ya wakilta wani ya yi masa yanka.

4) Idan wani mahajjaci ba ya da zarafin yin hadaya, sai ya yi azumin kwana goma; ukku daga cikinsu ya kasance an yi su ne a lokacin da a ke yin aikin Hajji, kuma ya fi kyau a yi su kafin ranar Arafah. Haka kuma an yarda mahajjaci ya yi azumin a cikin kwanaki ukku na Tashreeq. Sannan ya karasa sauran azumi bakwai bayan ya koma gida.

## 7- <u>Ranakun Tashreeq, me ya kamata mahajjaci ya yi a wadannan ranakun?</u>

Ranakun Tashreeq sune ranar sha daya, ranar sha biyu da kuma ranar sha ukku na watan Dhul-Hijjah. Mahajjaci zai aikata abubuwa kamar haka a wadannan kwanakin:

1) Zama a Mina a dararen wadannan kwanakin ukku; wannan zai samu ne kawai ta hanyar kasancewa a wurin na tsawon dararen saboda yana daya daga cikin wajiban aikin Hajji. Idan kuwa mahajjaci bai yi zaman daren Mina ba, kuma ba ya da wani kwakkwaran dalilin da ya hana shi, to ya aikata zunubi, don haka sai ya yanka dabba.

2) Yin jifar shedan sau ukku (karamar Jamrah, Jamrah ta tsakiya da babbar kuma babbar Jamrah) a lokacin da rana tayi Zawaali a kowace rana [na ukkun]. Sannan ya yi kowace sallah a cikin lokacin yin ta tare da gajarta salloli masu raka'o'i hudu zuwa raka'o'i biyu

## 8- <u>Tarbiyyar jifar shedan</u>:

A ranar goma shadaya ga wata, da tsakiyar rana, mahajjaci zai tsinci kankaru guda bakwai daga Mina ko akan hanyarsa ta zuwa can. Kowace kankara girmanta ya kasance kamar kwayar gida. Sannan ya mika zuwa karamar jamrah wurin da zai jefa kankara bakwai daya bayan daya, yana mai daga

hannu yana fadin "Allahu Akbar (allah Maigirma)". Mahajjaci ya tabbata cewa dukkan duwatsun da ya jefa sun fada a cikin kwandon jifa. Sannan sai ya doshi matsakaiciyar Jamrah wurin da zai jefa wasu duwatsun bakwai, daga nan kuma sai ya zarce zuwa ga babbar Jamrah ya jefa duwatsu bakwai. A rana ta goma sha biyu, ya maimaita hakan kafin rana ta yi zawwali. Babu laifi ga wanda ya hanzarta barin Mina a ranar sha biyu ga wata bayan faduwar rana. Wanda duk bai bar Mina ba kafin faduwar rana, to dole ne ya tsaya ya kashe dare a can, kuma zai jefi Jamrah ukku a lokacin Zawwali na rana ta goma sha ukku. Wannan ne ake kira "jinkiri" [watau jinkirtawa har sai rana ta goma sha ukku]. Kuma wannan yafi yin" gaugawar tafiya". Mata masu ciki da kananan yara da kuma tsofaffi wadanda suka kasa yin jifa da kansu, an yarda su wakilta wani ya yi ma su jifar. [1]

## **Ginshikan Aikin Hajji:**

---

[1] Mahajjacin da a ka ba wakilci sai ya fara yi wa kansajifa sannan yay i ma wanda ya ke yi ma wakilci a kowace Jamrah (babba, ta tsakya, karama) don kauce ma wahalarhar sai ya kammala ukkun sannan ya jefa ma wanda yak e wakilta.

Hajji na da ginshikkai hudu: yin Harami, tsayuwar Arafah, yin Dawafi da kuma yin Sa'y.

Hajji na da wajibbai bakwai: yin Harami daga Miqat, tsayuwar Arafah har faduwar rana, kashe dare a Muzdalifah, kashe dare a Mina a cikin kwanaki ukku na Tashreeq, yin jifar shedan, yin aski ko saisaye da kuma yin Dawafin Wadaa (Dawafin bankwana). Wanda duk ya bar daya daga cikin wadannan ginshikkan Hajjinsa bai inganta ba. A sabanin hakan, wanda duk ya bar daya daga cikin wajibbai to dole ne ya yanka dabba a Makka ya raba naman ga mabukatan da ke Massallaci Maitsarki ba tare da yaci wani abu daga cikin naman ba.

## 9- <u>Dawafin Wadaa':</u>

Idan mahajjaci ya kammala dukkanin ibadodin Hajjinsa, ya kuma bukaci komawa gida, to sai ya kewayi dakin Ka'abah sau bakwai, watau Dawafin Wadaa' ke nan, ba tare da ya yi Sa'y ba. In mahajjaci ya jinkirta Dawafin Ifaadhah da nufin ya yi shi kafin komawa gida, wannan ma ya isa. Matan da ke cikin jinin haila an dauke ma su yin Dawafin

Wadaa'; su na iya komawa gida ba tare da sun yi shi ba.

**Gargadi kan kura-kuran da wasu mahajjata ke tafkawa a lokacin yin ibadar Hajji:**

Wasu daga cikin wadannan kura-kuran da ake yi na da nasaba da Aqeedah (watau Imani) wasu kuma daga cikin na da nasaba da ka'idojin aikin Hajji. Game da wadanda suke da nasaba da imani, su ne kamar in mahajjata a garin Makka ko Madina sun ziyarci kaburbura don neman taimakon mutane mamata, su nemi albarka daga gare su ko su roki Allah don girmansu. Da duk dangogin shirka ko kirkire-kirkire ayukkan da suka saba ma koyarwar Annabi (S.A.W) a wurin ziyarar kaburbura. Wannan kuwa saboda Sunnar Annabi (S.A.W) ta dauki ziyarar kaburbura a matsayin wani abun tunatarwa game da ranar Alkiyama, da kuma yin addu'a ga Allah Ya yi ma mamatan rahama kuma Ya gafarta ma Musulmi mamata. Irin wannan ziyara tana da sharuddan da suka hada da cewa kar tafiyar ta kasance an yi ta ne musamman don ziyarar wadannan wuraren, kuma maza ne kawai suke zuwa

kamar yadda Annabi (S.A.W) yace, “A baya na hana ku ziyarar kaburbura, amma yanzu kuna iya ziyarar su, don hakika suna tunatar da ku ranar gobe kiyama.” Wannan Hadisin na magana da maza ne kawai, saboda Annabi (S.A.W) ya la’anci matan da ke yawan ziyarar kaburbura. Annabi (S.A.W) ya kan ziyarci kaburbura don ya roki Allah Ya yi ma mazaunan su rahama kuma Ya gafarta ma su. Wannan ita ce koyarwar Annabi Muhammad (S.A.W). A koyarwarsa, ana ziyarar kaburbura saboda al’amurra biyu, wadanda su ne; daukar gargadi da yin addua’a ga Allah Ya yi ma mamata rahama.[1]

Idan muka duba, za mu ga cewa ziyarar kaburbura da niyyar yin addu’a a wurin ko neman albarka ko taimako ko ceto daga mamaci ya saba ma koyarwar Annabi (S.A.W). Kuma wani nau’i ne na yi ma Allah kishiyoyi kuma hanya ce ta yin shirka; al’amarin da ya saba ma ibadodi da manufofin aikin Hajji.

---

[1] In mamatan Musulmi ne.

Wasu mahajjata suna wahalar da kansu da kuma bata lokacinsu da kudinsu wurin ziyarar ire-iren wadannan wuraren da ake kira wai wuraren kai ziyara a Makka da Madina. Ire-iren wadannan wurare a Makka su ne Kogon Hiraa, Kogon Thawr da wasu sauran wuraren da da ba a yi umurnin a ziyarta ba. A Madina kuma, akwai ire-iren wadannan wuraren kamar su; masallatai bakwai, masallacin Al-Qibla biyu da kuma wasu wurare da dama, don yin addu'o'i ko neman albarka daga wurinsu. Ziyarar wadannan wurare a Makka ko Madina don bautar Allah a cikinsu bidi'a ce da aka kirkira a Musulunci. Dalilin cewa haka kuwa shi ne babu wasu masallatan da aka yi umurnin a ziyarce su sai masallatai ukku kawai da aka ambata a cikin Hadisi: "su ne Masallaci Maitsarki, Masallacin Annabi (S.A.W) da kuma Masallacin Al-Aqsa." An kara da Masallacin Quba ne akan wadannan Masallatai ukkun da aka ambata a ciikin Hadisi ga mutanen da ke zaune a garin Madina kawai. Babu wasu wurare ko kogunan da a ka ce a ziyarta a

Makka ko Madina ko kuma wani wuri na daban[1] saboda babu wata hujja kan hakan. Kamar yadda mahajjata ke zuwa Makka don neman lada daga Allah, to dole ne su kiyaye abubuwan da Allah da ManzonSa suka yi umurni kansu.

Idan mahajjata sun yi tsimin lokacinsu wurin yin sallah a Masallaci Maitsarki da Masallacin Annabi (S.A.W) kuma sun yi tsimin kudinsu wurin kashe su ta hanyar Allah da yin sadaka ga talakwa da mabukata, to za su samu lada. Amma sabanin hakan, idan su ka bata lokacinsu da kudinsu wurin yin bidi'o'i da camfe-camfe za su samu hukunci (daga Allah). Don haka sai mahajjata su kula da wannan kuma kar su bi mutanen da ke kirkiro abubuwa ko jahilai. Kari kan haka kuma, kar su yarda a yaudare su da wasu karyace-karyacen bidi'o'i da aka tsara a rubuce a matsayin jagora kan ibadodi. A maimakon hakan, sai su koya daga sahihan jagororin ibadar da aka tattara ta hanyar amfani da Al'kurani Maigirma da kuma Sunnar Annabi (S.A.W) don kiyaye ingancin imaninsu. Kari

[1] Sai da kawai ziyartar kaburbura kana bun da a ka halatta kamar yadda aka yi bayani.

kan hakan kuma, mahajjaci ya kasance mai tambayar masana ilmi game da duk wani al'amarin dake daure masa kai.

**Kura-kuran da ke da nasaba da ibadodin aikin Hajji su ne:**

**Na farko: kura-kuran da a ke yi a wurin yin Harami:**

1) Wasu mahajjatan da ke tafiya a jirgin sama sukan yi jinkirin yin Harami har sai sun sauka filin jirgin Jeddah. Yin haka kuma kuskure ne don sun bar Miqat da su ka wuce a kan hanyarsu ta zuwa Makka. Annabi (S.A.W) ya yi bayani game da Miqat biyar da aka ambata, in da ya ke cewa, "Nasu ne, kuma na wadanda ke wuce su ne, kuma wadanda ba mutanen da ke zaune a wurin ba ne da suke da niyyar yin aikin Hajji da Umrah." Don haka duk wanda ya wuce ta Miqat ko yake hannun riga da ita a lokacin da ya ke saman jirgi sai ya yi Haramin Hajjinsa ko Umarah a wurin. Idan kuwa ya

bar Miqat ya yi Harami a wani wuri na daban, zai kasance mai zunubi saboda ya bar daya daga wajibban ibadodin aikin Hajji. Kan aikata hakan zai yanka dabba (fansar kai) domin kuwa Jeddah Miqat ce ta mutanen dake zaune cikinta kawai da wadanda ke da niyyar yin aikin Hajji ko Umrah a lokacin da suke cikin garin.

2) Wasu mahajjata sukan dauki hoton Haraminsu don tarihi. Suna ajiye irin wadannan hotunan don gwada ma abokansu; al'amarin da yake kuskure kan dalilai biyu:

Na farko, daukar hoto aiki ne na rashin da'a kuma babban zunubi don akwai Hadisan da suka zo da wannan hukuncin, da kuma bayanin hukuncin da za a yi ma mai aikata hakan. Kasancewar ka wanda ke saha'awar yin ibada, bai kamata ba ka fara yin wannan ibada da aikata zunubi ba.

Na biyu, wannan aikin Riya ne (kankanba) saboda mahajjaci nason mutane su ga hotonsa a lokacin da yake cikin Harami. An yi hani da aikata Riya kuma tana ruguza ayukka. Haka kuma, Riya

karamar Shirka ce (hada Allah da wani) kuma daya daga cikin ayukkan munafukai.

3) Wasu mahajjata suna tunanin cewa ya dace su zo da duk abun da suke bukata wurin yin Harami, kamar su takalmi silifa da kudi da kuma duk abubuwan da suka mallaka, kuma sun dauka cewar ba a yarda su yi amfani da duk wani abun da ba su suka zo da shi ba a lokcin yin Harami. Wannan tunanin kuskure ne, saboda mahajjaci ba ya bukatar yin kowane daga cikin wadannan. Ba a haramta masa yin amfani da abubuwan da ba shi ne ya zo da su ba lokacin yin Harami; hasali ma, an yarda ya sayi duk abun da yake bukata kuma ya yi amfani da duk abun da yake so. Haka kuma, an yarda ya canja kayan Haraminsa da wasu irinsu. Kari kan hakan kuma, an yarda ya canja takalminsa da wasu, an haramta masa kadai yin abubuwan da aka hana a yi cikin Harami.

4) Wasu mahajjata maza sukan bude kafadunsu a lokacin da suke yin Harami wanda yake

al'adar Idhtibaa' ce. An yarda a yi wannan al'adar ar ne kawai a lokacin aikata Dawafi (na Qodum ko na Umrah). A duk sauran lokutta, za a rufe kafada ne da Rida'. [1]

5) Wasu mata na tunanin cewa ya dace su yi Harami da koren sutura. Wannan tunani kuskure ne, saboda ba wata kayyadaddar kalar suturun da aka ce mata su yi Harami da su; hasali ma an yarda da su yi Harami a cikin suturarsu ta yau da kullum, amma ban da na ado ko masu matse jiki ko masu bayyana surarsu, saboda ba a yarda mace ta sa su ba a lokacin da take cikin Harami da kuma sauran lokutta.

6) Wasu mata na dora wani abu mai kama da rawani a saman kawunansu don su kare marafen fuskokinsu daga taba fuskokin nasu. Wannan kuskure ne, kuma babu wata hujja kan aikata hakan, saboda Hadisin da Aisha, Allah Ya yarda da ita ta ruwaito, ya bayyana cewa mata sukan rufe fuskokinsu a lokacin

[1] Saboda wannan yafi musamman a lokcin yin sallah

da suke cikin Harami don kauce ma kallon maza. Duk da haka, ba ta bayyana cewa suna sa rawani ko wani abu mai kama da shi ba. Amma babu laifi gare su in marfin fuskarsu ya taba fuskokinsu.

7) Wasu mata da ke cikin jinin haila sukan wuce Miqat ba tare da yin Harami ba, suna tunanin cewa tsarki na daya daga cikin sharuddan ingancin yin Harami. Wannan kuskure ne, saboda jinin haila ba ya bata yin Harami. a maimakon haka, an yarda mace mai haila ta yi Harami ta kuma yi dukkan ibadodin aikin Hajji, amma ban da Dawafi wanda za ta jinkirta har sai ta yi tsarki. Idan ta bar Miqat ba tare da yin Harami ba, to dole ne ta koma ta yo Haramin daga can, ko kuma ta yanka dabba a matsayin fansar kai, saboda ta bar wajibi.

**Na biyu: kura-kuran da ake yi a lokacin yin Dawafi:**

1) Mafi yawancin mahajjata suna dagewa kan yin wasu kebabbun addu'o'i wadanda suke karantawa daga jagoran ibada. Mafi yawancin lokutta, wani jagora yana karanta wadannan addu'o'in su kuma suna maimaitawa bayansa a tare. Wannan kuskure ne saboda dalilai biyu:

Na farko: wannan na daga cikin dagewa kan addu'a wadda ba Shari'ah ba ce ta aminta da shi, saboda Annabi (S.A.W) bai koyar da mu wasu kebabbun addu'o'in da za mu yi ba a lokacin da muke gudanar da Dawafi.

Na biyu: yin addu'a ga Allah a tare Bidi'ah ne, kuma yin hakan na damuwar wasu mahajjata tare da kawar masu da hankali. Abun da aka halatta shi ne kowane mahajjaci ya yi wa kansa addu'a ba tare da ya daga murya ba.

2) Wasu mahajjata suna sumbatar Kusurwar Yamaani. Wannan kuskure ne, saboda an yarda a taba ta ne kawai, amma Bakin Dutse ne kawai aka yarda a sumbata. Ana taba Bakin Dutse ko sumbatar sa in an samu damar yin hakan. Amma idan har akwai cinkoson mutane, sai mahajjaci ya nune shi. Ita Kusurwar Yamaani taba ta ne kawai a ke yi; ba a sumbatar ta kuma ba a nunin ta saboda an kasa kaiwa gare ta don cinkoso mutane kamar yadda ake yi ma Bakin Dutse. Sauran kusurwoyin kuma ba a taba su kuma ba a sumbutar su.

3) Wasu mahajjata sukan turi mutane don sukai ga Bakin Dutse su taba shi kuma su sumbace shi. Ba a yarda da yin haka ba, saboda cinkoson mutane na da wuya da matukar hatsari, kuma akwai Fitina (jaraba) irin ta shedan a wurin da ake turereniya a tsakanin maza da mata. Abun da kawai aka halatta a wurin shi ne tabawa da sumbatar Bakin Dutse, ko wannan sai in da halin yin hakan fa. Amma idan ba halin yin hakan, nunin sa

kawai ya isa ba tare da an turi jama'a ba, kutsa kai cikin hatsari (ba da gangan ba) yana jawo sha'awar mata. Haka kuma, ayukkan ibada ana yin su ne a saukake cikin natsuwa, musamman ma cewa ana tabawa da sumbatar Bakin Dutse kawai ne in an samu damar yin hakan. Amma in ba a samu damar yin hakan ba, to sai a nune sa kawai, don haka turin wasu don aikata hakan zunubi ne. To ta yaya mahajjaci zai aikata zunubi don ya samu ladar aikata Sunnah.

**Abu na ukku: kura-kuran da ake yi a wurin yin saisayen gashi bayan an gama aikin Hajji ko Umrah**:

Wasu mahajjata sukan datse wani bangare na gashinsu ne kawai, wanda yin hakan bai isa ba kuma bai cika ibadar ba. Dalilin cewa haka kuwa shi ne, yin saisayen gashi na nufin a saisaye kai ko'ina saboda yin haka maye gurbin aske gashin kai ne kwaca-kwam. Saboda haka saisayen gashi zai game kai gaba daya. Allah Madaukakin Sarki Na cewa: ﴿مُحَلِّقِينَ رُءُوسَكُمْ وَمُقَصِّرِينَ لَا تَخَافُونَ﴾ [48: 27]. "Wanda

duk ya datse wani sashen gashinsa, ya saisaye wani bangaren gashinsa ne kawai ba dukan kansa ba.”

**Abu na hudu: kura-kuran da ake yi a lokacin tsayuwar Arafah:**

1) Wasu mahajjata ba su da yakinin wurin yin tsayuwar Arafah, kuma ba su la’akari da alamu da suke nuna Arafah; don haka suna tsayawa ne a wajen Arfah. Wanda duk ya aikata haka kuma bai tsaya a cikin harabar Arafah ba, Hajjinsa bai inganta ba. Dole ne mahajjaci ya kula da wannan al’amari, ya kuma tabbata ya tsaya a cikin harabar Arafah.

2) Wasu mahajjata na da imanin cewa dole ne a gani ko a hau dutsen Ar-Rahma. A sakamakon hakan, sukan sa kansu cikin hatsari don su aikata wannan, duk da yake ba a bukatar yin hakan. Abun da yake wajibi shi ne tsayuwar Arafah, saboda Annabi (S.A.W) yace, “Dukkan Arafah wuri ne na tsayuwa, amma kar ku shiga cikin Uranah.” Ko da

kuwa suna ganin dutsen ne ko ba su ganin sa a lokacin da suke yin addu'a. Abun da ake bukata kawai shi ne mutum ya fuskanci Ka'abah (alqibla).[1]

3) Wasu mahajjata sukan bar Arafah kafin faduwar rana wanda ba a yarda da yin hakan ba, saboda lokacin faduwar rana ne ke tabbatar da lokacin barin Arafah. Duk wanda ya bar Arafah kafin wannan kayyadadden lokaci zai yi yanka don fansar kai saboda yabar daya daga cikin wajiban aikin Hajji. An samo wannan kayyadadden lokaci ne daga aikatawar Annabi Muhammad (S.A.W), wanda ya tsaya a Arafah har faduwar rana. Manzon Allah (S.A.W) yace "ku koyi yanda za ku yi ibada daga re ni".

**Na biyar: kura-kuran da ake yi Muzdalifah:**

A lokacin da mahajjaci ya isa Muzdalifah, zai yi sallar huturu da ta dare a hade. Zai kashe dare a wurin sannan ya yi ta yin addu'a ga Allah har

[1] Dutsen ba Al-Qibla bane.

zuwa wayewar gari. Bayan haka sai ya bar wurin zuwa Mina. Mahajjatan da suke da dalilai masu karfi musamman mata da tsofaffi da kananan yara da masu kula da su an yarda su bar Mina bayan dare ya raba.

Duk da haka akwai kura-kuran da a ke yi a cikin wannan ibadar saboda wasu mahajjata ba su hakikancewar ko suna a harabar Muzdalifa ko kuwa a'a; sai su kashe dare a bayanta. Sauran mahajjata sukan bar Muzdalifah kafin dare ya raba, kuma ba su kashe dare a wurin. Duk wanda bai kashe dare a Muzdalifah ba, ba tare da wani kwakkwaran dalili ba, to zai yi yanka don fansar kai, kuma akwai bukatar ya tuba ya roki Allah Ya yafe masa saboda ya bar daya daga cikin wajibban Hajji.

**Na shidda: kura-kuran da ake yi a wurin jifar shedan:**

Jifar shedan daya ne daga cikin wajibban aikin Hajji. Mahajjaci zai yi jifar Jamratul-Aqbah a ranar Idi da kuma Jamaraat ukku (karama-matsakaiciya-babba) a cikin ranakun Tashreeq.

Jamratul-Aqbah na farawa ne daga rabawar daren ranar Idi, a yayin da Jamaraat ukku za a jefe su a lokacin da rana ta yi Zawaali (idan rana ta yi sanyi) a ranakun Tashreeq. Wasu mahajjata na aikata kura-kurai a wurin yin wannan ibadar, kura-kuran su ne:

1) Wasu mahajjata sukan yi jifa a duk lokacin da suke bukata ba tare da kula da kayyadadden lokacinsu ba, watau su yi jifa kafin rabawar daren Idi ko su jefi Jamaraat ukku kafin lokacin Zawaal a cikin ranakun Tashreeq. Duk wanda ya yi jifa kafin kayyadadden lokacin yin ta ba za a karbi jifarsa ba, kamar dai hukuncin wanda ya yi sallah kafin lokacin yin ta.

2) Wasu mahajjata ba su tsare ka'idar tsarin jifar Jamarat, watau farawa da babba ko na tsakiya. Wannan kuskure ne, saboda kamata ya yi mahajjata su fara da karamin sannan na tsakiya sannan daga karshe a kai ga babba.

3) Wasu mahajjata sukan yi jifa ta fada ba a cikin kwandon Jamrah ba, idan sun yi jifa daga nesa duwatsun ba za su fada a cikin

kwandon Jamrah ba. Don haka ba za a sa wannan a cikin lissafi ba, kuma dole ne mahajjaci ya sake wannan saboda duwatsun da ya jefa ba su fada a cikin kwandon Jamrah ba. Dalilin yin wadannan kura-kuran shine jahilci ko gaugawa ko kuma rashin natsuwa.

4) Sauran mahajjata sukan yi jifar ranar Tashreeq ta biyu da ta ukku a ranar farko, sannan su yi tafiya ba tare da sun kammala ibadar Hajjinsu ba. Saura mahajjatan kuma sukan yi jifar ranar Tashreeq ta farko kawai sai su wakilta wani ya yi masu sauran jifar don su koma gida. Wannan na daga cikin kinayar da ake yiwa ibadar Hajji, kuma wannan aikin shedan ne, saboda mahajjaci ya kashe dukiyarsa kuma ya wahalar da kansa don yin aikin Hajji. Sai ga shi a lokacin da yake gab da ya kare sauran ibdodin da suka rage masa, shedan ya ribance sa don ya bar wasu daga cikin wajibban aikin Hajji, kamar kammala jifar shedan, kashe dare a Mina a ranakun Tashreeq da yin Dawafin Wadaa' a lokacin da ya dace a yi shi. Saboda

kayyadadden lokacin yin Dawafin Wadaa' shi ne bayan ibadar kashe dukkanin dararen Hajji da kuma kammala dukkanin ibadodin aikin Hajji. Zai fi kyau gare sa idan ya yi tsimin kudinsa da lokacinsa da kokarinsa, a maimakon bata su ba tare da kammala ibadarsa ba. Allah Madaukakin Sarki Yace:[1] ﴿وَأَتِمُّوا الْحَجَّ وَالْعُمْرَةَ لِلَّهِ﴾. A cikin wannan aya, "kammala Hajji da Umrah" na nufin kammala dukkanin ibadodi ga dukkan wanda ya daura Harami cikin gaskiya ya yi niyyar yin Hajji don samun yardar Allah.

5) Wasu mahajjata ba su fahimci ma'anar "gaugawa" ba wadda anka ambata a cikin ayar da Allah Madaukakin Sarki ke cewa: ﴿فَمَن تَعَجَّلَ فِي يَوْمَيْنِ فَلَا إِثْمَ عَلَيْهِ وَمَن تَأَخَّرَ فَلَا إِثْمَ عَلَيْهِ﴾ Sun yi kuskuren fahimtar cewa "gaugawar tafiya cikin kwana biyu" na nufin ranar Idi da kuma rana ta biyu; sai su tafi a ranar sha daya ga watan Dhul-Hijjah, suna cewa wai suna sauri su tafi gida. Wannan

[1] [2: 196]

kuskure ne baki daya, saboda kwana biyu na nufin ranar sha daya da ranar sha biyu. Don haka, babu laifi ga duk wanda ya hanzarta tafiya gida bayan ya yi jifa, bayan lokacin Zawaalin rana ta goma sha biyu. Duk da haka, an ba da zabi ga duk wanda ke bukatar ya jinkirta tafiyarsa har zuwa ranar sha ukku ga wata, sannan ya koma gida bayan ya yi jifa bayan rana ta yi Zawaali.

**Na bakwai: kura-kuran da ake yi a lokacin ziyarar Masallacin Annabi (S.A.W):**

Babu shakka ziyarar Masallacin Annabi (S.A.W) aiki ne na Sunnah, kamar yadda Annabi (S.A.W) yace: "Mutum zai yi tafiya ne don Masallatai ukku kawai, masallatan su ne: Masallaci Maitsarki, Masallacina da kuma Masallacin Al-Aqsa" Kuma Manzon Allah (S.A.W) ya sanar da mu cewa yin sallah a masallacinsa yafi yin sallah sau dubu a wani wuri na daban da Masallaci Maitsarki. Wannan hujja ce da ta nuna yarda a yi tafiya don kai ziyara ga masallacin Annabi (S.A.W) mai albarka.

Duk da haka wasu mahajjata suna aikata kura-kurai game da wannan al'amarin kamar haka:

1) Wasu mahajjata sun yi imanin cewar ziyarar Masallacin Annabi (S.A.W) wani bangare ne na aikin Hajji. Wannan imanin nasu kuskure ne babba, saboda ba a kebe wani lokaci na musamman ba a cikin shekara don ziyarar Masallacin Annabi (S.A.W) kuma ba ya da wata nasaba da aikin Hajji. Don haka duk wanda ya yi Hajji ba tare da ziyarar Masallacin Annabi (S.A.W) ba Hajjinsa ta inganta.

2) Wasu sunyi imanin cewa ziyarar Masallacin Annabi (S.A.W) wajibi ne. Wannan imanin ba gaskiya ba ne saboda ziyarar Masallacin Annabi aikin Sunnah ne. Babu laifi ga Musulmin da bai ziyarci Masallacin Annabi (S.A.W) ba a lokacin rayuwarsa. In muka duba za mu ga cewa wanda duk ya kai ziyara zuwa Masallacin da niyya mai kyau zai samu lada babba.

3) Wasu mahajjata suna tunanin cewa ziyarar Masallacin Annabi na nufin ziyarar Annabi (S.A.W) ne shi kansa, ko kabarinsa. Wannan imanin kuskure ne saboda tafiyar da aka yarda da ita kawai ita ce, wadda aka yi zuwa Masallacin na Annabi don a yi sallah a wurin. Amma ziyarar kabarin Annabi (S.A.W) da wasu kaburburan Sahabbai da shahidai an sa ta cikin ziyarar Masallacin ne, amma ba a kulla tafiya ba saboda ziyarar kaburburan ba kawai. Dalili kuwa shi ne, Annabi (S.A.W) ya hana yin tafiya da niyyar yin ibada a ko'ina in ban da masallatan ukku (da aka bayyana a cikin Hadisi). Don haka, ba a yarda a yi tafiya ba don kawai ziyarar kaburburan Annabawa da Waliyyai. Haka kuma, an hana yin tafiya zuwa wani masallacin da ba ya cikin ukkun da aka ambata don yin sallah. Game da hadissan da aka ba da a ka kafa hujjar ziyarar kabarin Annabi (S.A.W) da su, ba su da karfi ko kuma kirkirarru ne kamar yadda manyan Imamai suka bayyana da malaman Hadissai.

Duk da haka, an so duk wanda ya ziyarci Masallacin Annabi (S.A.W) ya ziyarci kabarinsa da na Sahabbansa a lokacin ziyarar Masallacin. An yarda da yin haka, kan dalilin cewa ziyarar kaburbura baki daya halat ce idan da niyyar aikawa da aminci zuwa ga mamata da kuma rokon Allah Ya yi ma su rahama ne. Sabanin haka, ziyarar kaburbura da niyyar neman taimakon daga mamata ko rokon su biyan wata bukata shirka ce wadda ba a yarda da ita ba.

4) Wani daga cikin kura-kuran da wasu ma su ziyarar Masallacin Annabi (S.A.W) mai albarka suke yi shi ne imani da cewa sai sun yi wasu kayyadaddun raka'o'in salloli, kamar yin sallah arba'in da sauransu. Wannan kuskure ne don ba a taba bayar da rahoton cewa Annabi (S.A.W) ya kayyade yawan sallah ga wani wanda ya ziyarci masallacinsa ba. Kari kan haka kuma shi ne, Hadisin da ya yi bayanin sallah arba'in kirkirarre ne kuma ba ya da inganci, don haka ya kamata Musulmi ya yi sallah

gwargwadon yadda ya ke iyawa ba tare da wani shamaki ba.

5) Wani daga cikin manyan kura-kuran da wasu ma su ziyarar kabarin Annabi su ke yi shi ne daga muryoyinsu a lokacin da suke yin addu'o'i a kusa ga kabarinsa. Saboda sun yi imanin cewa yin addu'a kusa ga kabarinsa na da daraja kuma an yarda da yin hakan. Wannan gaba daya kuskure ne saboda ba a yarda a yi addu'a zuwa ga Allah ba kusa ga kaburbura, ko da kuwa mutum ya roki Allah ne shi kadai kawai, wannan Bidi'ah ce kuma hanyar yin shirka. Bugu da kari kuma, magabatanmu da ke kan hanya madaidaiciya ba su yi addu'a ga Allah ba kusa ga kabarin Annabi (S.A.W); maimakon yin hakan, sukan aika ma sa da amincinsu, sannan kuma su tafiyar su. Don haka, wanda duk ke son ya yi addu'a ga Allah kamata ya yi ya fuskanci Alkibla, kuma ya aikata hakan a cikin masallaci ba kusa ga kabari ba. Saboda Alkiblar addu'a ita ce Ka'abah mai albarka, don haka sai a kiyaye.

Wani babban kuskuren da ma su ziyarar Masallacin Annabi (S.A.W) su ke yi kuma shi ne suna zuwa ziyarar wasu wurare da masallatai a Madina da ba a yarda a ziyarta ba. Alhali kuma ziyarar irin wadannan wuraren al'amarin Bidiah ne da aka haramta. Misalan ire-iren wadannan wuraren su ne; masallacin Al-Ghamaamah, masallacin Al-Qibla biyu, masallatai bakwai da wasu ire-iren wadannan wuraren da wasu jahilai da wasu 'yantsirarun mutane su ke dauka a matsayin wuraren da a ka yarda a ziyarta. Wannan daya da cikin manyan kura-kurai ne saboda babu wani masallacin da a ka yarda a ziyarta a Madina da dalilin yin sallah a wurin sai Masallacin Annabi (S.A.W) da Masallacin Quba. Game da sauran masallatai da ke Madina, darajarsu kamar ta sauran masallatan da ke fadin duniyar nan ne, ba wanda yafi wani daraja a cikinsu.

Don haka, sai Musulmi su kiyaye wannan kuma su guji bata dukiyarsu da lokacinsu ga al'amurran da za su gusar da su daga [hanyar Allah] Allah da rahamaSa. Saboda duk wanda ya yi wani aikin da Allah ko AnnabinSa ba Su umurce sa da yi

ba, to ba za a karbi aikin nasa ba, kuma zai kasance mai zunubi, saboda Annabi (S.A.W) yace: "Wanda duk ya yi wani abun da ba mu umurce sa da yi ba, to ba za a karbi aikin ba." Daga cikin abubuwan da Annabi (S.A.W) ya fadi ko ya aikata babu wata hujjar da ta nuna yarda da ziyarar masallatai bakwai, masallacin Alkibla biyu da masallacin Al-Ghamamah. Hasali ma, kirkirarrar Bidi'ah ce wadda ya kamata a guje ta.

Muna rokon Allah Madaukakin Sarki Ya ba mu ikon ganin gaskiya a matsayin gaskiya, Ya kuma ba mu karfin bin ta da dagewa kanta; Ya kuma ba mu ikon ganin karya a matsayin karya, kuma Ya ba mu karfin guje ma ta. Yabo ya tabbata ga Allah, Ubangijin duniyoyi, aminci da albarkokinSa su tabbata ga Annabi Muhammadu (S.A.W) da iyalansa da Sahabbansa.